Kowa ne aikin alheri sadaka ne

Daga Jabir ɗan Abdullahi - Allah Ya yarda da su - daga Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi - ya ce: "Kowa ne aikin alheri sadaka ne".
[Ingantacce ne] [Bukhari ne ya ruwaito shi daga hadisin Jabir, kuma Muslim ya ruwaito shi daga hadisin Huzaifa]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi - yana ba da labarin cewa dukkanin kyautatawa da amfani ga wasu na magana ne, ko na aiki yana zama sadaka, kuma a cikinsa akwai lada da sakamako.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/5346